Cewa Manzan Allah-tsira da Amincin Allah su tabbata agareshi-yayi Zobe na Zinare

An karbo daga Abdullahi Dan Umar-Allah ya yarda dasu-"Cewa Manzan Allah-tsira da Amincin Allah su tabbata agareshi-yayi Zobe na Zinare,ya kasance idan zai sashi yana sanya kansa acikin tafinsa,sai Mutane sukai hakan,sannan cewa ya zauna akan Minbari sai ya cireshi yace:Hakika na kasance ina sanya wannan Zoben,kuma ina sanya kansa daga ciki,sai ya yar dashi sannan yace:Na rantse da Allah bazan kara sashi ba har abada sai Mutane suka jefar da Zobunansu".A wani Lafazin"Ya sanya shi a Hannunsa na Dama".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi tshira da amincin Allah su tabbata agareshi yayi Umarni ai masa Zoben Dinare,ya kasance idan zai sashi yana sanya kansa cikin Tafinsa,sai Sahabbai suka bishi akan haka sukayi kamar yadda yayi,sannan bayan wani Lokaci Annabi tshira da Amincin Allah su tabbata agareshi ya zauna kan Minbari don Mutane su ganshi,sannan yace:Hakika na kasance ina sanya wannan Zoben,kuma ina sanya kansa acikin Tafina,sannan ya yarda shi yace:Na rantse da Allah bazan kara sashiba har abada,wannan ya faru ne bayan an haramtashi,sai Sahabbai suka jefar da Zobunansu saboda koyi da Manzan Allah tshira da amincin Allah su tabbata agareshi

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2951